# Bege na Gaskiya ga Kaunatattunka da Suka Mutu (Sashe na 1)

An dauko daga babi na 7 na littafin nan *Menene Ainihi Littafi Mai Tsarki Yake Koyarwa?* za a iya samunsa a dandalin jw.org/ha.

**MANUFA: Ka bincika abin da ka yi imani da shi da kuma dalilin da ya sa ka yi hakan kuma ka bincika abin da Littafi Mai Tsarki ya koyar don ka iya bayyana wa wasu abin da ka yi imani da shi.**



## ANYA ZA MU DAINA YIN BAKIN CIKI SABODA KAUNATATTUNMU DA SUKA MUTU KUWA?

### 1 KA BINCIKA ABIN DA KA YI IMANI DA SHI

Me ya sa wasu za su iya ce a'a?

______________________________

______________________________

Me ya sa wasu za su iya ce e?

______________________________

______________________________

Me *ka* yi imani da shi?

______________________________

Me ya sa ka yi imani da hakan?

______________________________



www.jw.org/ha © 2015 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania

## 2 KA BINCIKA ABIN DA LITTAFI MAI TSARKI YAKE KOYARWA

**Ba laifi ba ne mutum ya yi kuka sa'ad da wani wanda yake ƙauna ya mutu.**
(Ka duba babi na 7, sakin layi na 1-6 na littafin nan *Menene Ainihi Littafi Mai Tsarki Yake Koyarwa?*)

### Karanta 1 Korintiyawa 15:26.

Idan mutuwa maƙiya ce a gaban Allah, kana ganin cewa zai tsauta mana idan muka yi baƙin ciki saboda hakan? Me ya sa hakan zai yiwu ko ba zai yiwu ba?

________________________________________

________________________________________

________________________________________

### Karanta Yohanna 11:33, 35; 14:9.

Yaya Jehobah da kuma Yesu suke ji game da baƙin ciki da muke yi sa'ad da wanda muke ƙauna ya mutu?

________________________________________

________________________________________

________________________________________



**Kamar yadda rana take fitowa bayan hadari, haka ma za mu yi murna kuma mu daina yin baƙin ciki sa'ad da aka ta da waɗanda muke ƙauna daga mutuwa**


www.jw.org/ha © 2015 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania

## A lokacin tashin matattu, za mu daina baƙin ciki kuma za mu yi murna.

(Ka duba babi na 7, sakin layi na 7-10 na littafin nan *Menene Ainihi Littafi Mai Tsarki Yake Koyarwa?*)

**Karanta Luka 8:40-42, 49-56; Yohanna 11:43, 44.**

Ta yaya Yesu ya nuna cewa idan wani wanda muke ƙauna ya mutu, hakan ba ya nufin cewa ba zai sake rayuwa ba?

**Karanta Markus 5:42.**

Ta yaya wannan ayar ta ba mu ƙarin haske game da yadda za mu ji sa'ad da aka yi tashin matattu a nan gaba?

Yaya kake ji sa'ad da ka san cewa za a tayar da ƙaunatattunmu da suka mutu kuma za mu daina yin baƙin ciki?


www.jw.org/ha © 2015 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania

## 3 KA BAYYANA ABIN DA KA YI IMANI DA SHI

IDAN WANI YA CE…

**Idan mutum yana baƙin ciki, hakan yana nufin bai gaskata cewa za a yi tashin matattu ba.**

ZA KA IYA CE…

**Mai yiwuwa mutane da yawa za su yarda da hakan. Amma ban gaskata da hakan ba domin…**

________________________________________

________________________________________

Wane nassi ne za ka iya karanta wa mutumin?

________________________________________

Bisa ga ra'ayin mutumin, ta yaya za ka bayyana wannan nassin?

________________________________________

IDAN WANI YA CE…

**Idan mutane suka mutu, ba za su sake rayuwa ba.**

ZA KA IYA CE…

**Idan waɗanda muke ƙauna suka mutum, gaskiya ne cewa sun daina rayuwa. Amma na gaskata cewa za su sake rayuwa a nan gaba domin…**

________________________________________

________________________________________

Wane nassi ne za ka iya karanta wa mutumin?

________________________________________

Bisa ga ra'ayin mutumin, ta yaya za ka bayyana wannan nassin?

________________________________________


www.jw.org/ha © 2015 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania